## 1. KA 'IDODIN GUDANAR DA HARKAN ZIYARCE ZIYARCEN KASASHE DA AKA ZARTAR SUNE HAKA:

MATASHI

Mu, jami 'an hukumar kula da harkan ziyara na kasashen duniya (tana kunshe ne da jama 'an kasashe daban daban da kuma jama'an ma'aikatoti na ziyara da kungiyoyi masu kama da haka) munyi zaman Babban majilisan kungiyanmu a garin santiago, kasar chile, daya ga watan 10 na 1999.

Muna kara jaddada rukuni na uku na makasudin kafa hukumar ziyara ta duniya tare da la 'akari da rawan gani da hukumar take takawa wanda majalisar dinkin duniya tayi na 'am da shi wanda ya kunshi daukaka hidiman ziyaran kasashen duniya wanda sakamakonsa kuwa shine: Kawo hadinkan duniya baki daya, tare da raya zaman lafiya,

da kuma kula da yancin kan jama'a ba tare da gwada banbanci ba wajen launin fata, ko yare, ko kuma addini ko kuma jinsi.

Mun yi kuma imani da cewa mu'ammalar da ziyara yake kawowa tsakanin jama'u na duniya wadanda yarensu da yanayin rayuwansu yayi daban da na juna shine babban makamin da zai haddasa abokantaka da kuma jituwa tsakanin kasashen duniya.
Muna kuma amincewa da hukumar majalisar dinkin duniya game da ra'ayoyinta wajen yaki da talauci, kawo cigaban tattalin arziki, da lura da muhallin kasa d. s. s. a taron da suka yi a Rio de Janeiro.

Muna kuma yin la 'akari da cigaban tattalin arzikin kasashe da kuma cigaban rayuwa da aka samu da, da kuma wanda ake tsammanin samu saboda bunkasan da aka samu wajen harkokin ziyara wanda ana yinshi ne don jin dadi, ko don cinikayya, ko don raya al'adu, ko don addini, ko don kula da lafiya ko da yake dai shi harkan ziyara kamar komai a duniya yana da nashi koma bayan.
Ci gaban nan dai ana samu ne a sashen kasan da aka ziyarta da kuma kasar su maziyartan, Birni da kauye.

Muna da niyyan mu mara baya ma tsarin ziyara da zai bama kowa 'yancin yin tafiya domin ziyaran kasashen da ya ga dama, a lokacin da ya samu yayi haka ba tare da samun matsala ba.

Mun kuma yarda da cewa ita mu 'amalar ziyara ta kasashen duniya zata samu amfani kwarai da gaske muddin dai rayuwar ta yana kawo rayawar cinikayya da sana'oi.

Mun kuma tabbatar da cewa mudin akwai wadansu ka 'idodin da hukunce – hukunce da ke kula da tafiyar da harkan ziyara, to wannan yanayin zai kawo hadewan kai wajen

gudanar da cinikayya wanda yana daya daga cikin abunda yasa aka kafa hukumar ziyara ta duniya.

In anyi lura da haka kuwa za a gane cewa lalle ne dukkan masu fadi aji na harkar ziyara, wanda ya kunshi jami 'an wannan aiki daga karkara har zuwa na kasa baki daya, kungiyon yan kasuwa na duniya da dukkan sauran kamfanoni da hukumomi masu mu 'ammala da harkan ziyara suna da nauyin da zasu dauka da kuma rawan da zasu taka wajen ganin cewa an cimma burin da yasa aka kafa hukumar ziyara ta duniya.

Muna kuma masu bin umurnin makasudin da hukumar kula da harkan ziyara ta duniya take kokarin cimmarwa ta wajen kawo hadin hannu tsakanin mutanen da suke cin gashin kansu a harkan ziyara da kuma jami'an gwamnati, da kuma kawo hadin gwuiwa tsakanin kasan masu ziyara da kuma kasan da ake ziyarta. An zayyanar da wannan makasudin ne a zaman majalisar hukumar wanda akayi a garin Istanbul a shekara 1997.

Mun kuma yi na'am da a ci gaba da aiwatar da shawurwuran da aka dauka a shekara 1997 a garin Sofia wanda yake magana akan amfanin ziyara ga rayuwar dan Adam. Ammana kuma ya zama dole ne wadannan shawurwuran su samu marawan baya da wadannan su ka 'idodin masu Karin bayani wanda masu tafiyar da harkan ziyara zasu kera yadda yanayin al 'ammuran su zai kasance a cikin karni na ashirin da daya.

Yin haka kuwa zai kunshi amfani da irin bayani da aka yi ma wasu lakabi kamar "Bako", "Maziyarci", "Ziyara" wanda kowannensu yana da nashi nufin.

Wadannan bayanan anyi su ne a garin Ottawa tsakanin 24 zuwa 28 ga watan yuni 1991 wanda kuma aka zartar 'a matsayin jagora ga harkan ziyara a Amurka a yayin zaman hukumar su ta kidaya.

Ababen da suka tattauna sun hada da:

- Hukuncin da aka zartar akan 'yancin kai wanda aka yi ranar 10 ga watan dicemba a shekar 1948.
- Yarjejjeniya akan yancin wajen harkan cinikayya da gudanar da ababen al 'adu a ranar 16 ga waten Dicemba a shakara 1966.
- Yarjejjeniya akan yancin kai wajen al'amuran siyasa da aka yi a ranar 16 ga watan Dicemba shekara ta 1966.
- Taron da aka yi a Warsaw akan al 'ammuran tafiye – tafiye na jirgin sama.
- Taron da aka yi a Chicago ranar 7 ga watan Dicemba shekara 1944 da kuma a Tokyo, da kuma Montreal duk a kan huldan tafiya da jirgin sama.
- Taron da aka yi don kare gargajiya da al 'adu na kasashen duniya baki daya da aka yi ranar 23 ga watan Nuvemba shekara 1972.
- Taron da aka yi a Manila akan hukumar ziyara ta kasashen duniya baki daya a 10 ga watan goma a shekara ta 1980.
- Hukunci da aka yanke a zama ta 6 na majalisar hukumar ziyarce – ziyarce a garin Sofia wanda aka zartar da ka 'idodin da kuma tsarin ziyara a rana 26 ga watan satumba na 1985.
- Taro akan kare hakkin yara a ranan 26 ga watan janeru a 1990.
- Zaman da majalisar hukumar ziyara tayi a garin Buenos Aires akan yadda za 'a inganta ziyara tare da samar da isassun matakan tsaro domin kare lafiyan masu tafiya wanda aka yi ranan 4 ga watan October a 1991.
- Tattaunawan da aka yi a garin Rio ranan 13 ga watan yuni a 1992 akan inganta muhallen ziyara a kasashen duniya baki daya.
- Yarjejjeniyan da aka yi, 15 ga watan Aprilu a 1994 akan yadda za 'a tafiyar da cinikayyar ayyuka a tsakanin kasashen duniya.
- Hukuncin da aka zartar akan yadda za' a hana ziyara dan karuwanci a zaman majalisar ta 11 wanda aka yi a Cairo ranan 22 ga watan Octoba a 1995.

- Taro akan yadda za a kara haddasa auratayya tsakanin jama 'un kasashen duniya ranan 6 ga watan janeru a 1995.
- Hukuncin da aka zartar akan hana tilasta yara yin karuwanci wanda akayi a Stockholm a watan Agusta 1996.
- Taro akan nazarin yadda ziyara yakan inganta yanayin rayuwa da al 'adun jama'a a ranan 22 ga watan mayu a 1997.
- Shawarwarin da hukumar tarayyan ma 'aikata ta duniya baki daya ta kaddamar, wadanda suka shafi kare hakkin ma 'aikata, da hana tilasta ma yara yin aiki dole don kudi da kuma tattabar da hana nuna bambamce-bambamce a wurin aiki.
- A bisa duk wadannan ababen da muka yi ta lissafawa, muna kara jaddada yanci da maziyarci yake da shi a wajen ziyara a ko 'ina a duniya.

Muna kuma ayyanar da niyyan mu ta ganin cewa mun kafa tsari a hidiman ziyara wanda za 'a iya aikatarwa kuma wanda zai kawo daidaituwa tsakanin al 'umma wanda ko wani sashe na jama 'a.

Muna kuma rantsar da wadannan ka 'idodin kamar haka :

**TSARI**

**Rukuni na 1**

**Gudumarwa da ziyara ke kawowa wajen kawo fahimtan juna da karimci tsakanin kasashen duniya:**

(1) Ginshikan ziyara dai suna gine ne a kan kawo fahimtan juna tsakanin jama 'u musamman ta wajen bambanci wajen adabi da addini da dai sauran al 'adu na yau da kullum. Saboda haka dole ne masu ziyara da kuma sauran masu cin amfanin sa su girmama kuma su karimta al 'adun jama 'un da suke hulda da su.

(2) Ya zama dole ma mai ziyara yayi ziyaransa ba tare da ya saba ma dokoki ko al 'adu ko addini ko wani abu dai na kasan da yake ziyara.

(3) Su kuma ma 'aikatan harkokin ziyara na kasan da ake ziyarta dole ne su yi nazari su sami ilimi akan yadda al 'adun su masu ziyaran suke. Wannan kuwa shi zai taimaka wajen yadda ma 'aikatan zasu tafiyar dasu yadda ya kamata.

Ya zama wajibi akan ma 'aikatan su tabbatar da karewan lafiyan masu ziyaran da su da dukiyansu musamman maziyartan da suke daga kasashen waje; kuma dole ne a yi hukunci mai tsauri akan wadanda suka yi sakaci akan haka.

(5) Dole ne suma masu ziyaran su kare kansu daga shiga uku. Su tabbatar da sun yi biyayya ga dokokin kasan da suka ziyara.

(6) Ya kamata baki da maziyarta su nemi sani isashshe akan kasan da zasu ziyarta saboda su san yadda zasu kare kansu ta wajen cututtuka da sauran ababen da zasu iya kawo rauni.

**Rukuni na 2**

**Ziyara a matsayin garkuwan da zai iya kawo cikon burin kai.**

(1) Ziyara dai an sani wani abu ne da za 'a danganta shi da kamar nishadi ko shakatawa. Idan kumo aka yi nazarinsa sosai aka tsarai shi yadda ya kamata aka kuma aikata shi da zuciya daya, to ba shakka zai zame ma mutum wani babban arziki ne wanda zai samar ma mutum ilimi da kuma sanin yadda za'a zauna da jama'a iri–iri.

(2) Kada ziyara ta gwada bambancin jinsi. Ya kamata ta inganta karimci da zumunci tsakanin juna, ta kuma yi kokari wajen kare hakki da yancin sashoshin da basu iya kula da kansu Kaman yara da tsofi da nakasassu.

(3) Matsarwa musamman ma yara wajen sasu yin karuwanci bai yi daura da koyarwan ziyara ba. Saboda haka dole ne ma 'aikatan su nemi taimakon hukumomi na kasashe wajen ganin cewa sun hanar da wannan mummunan aikin.

(4) Mara baya ma ziyara don addini ko don neman ilimi ko don neman lafiya ko don koyon yare d. s. s. ya zama wajibi domin kuwa suna kawo ci gaba iri – iri.

(5) Ya kamata a koyar da amfanin ziyara a makarantu da ci gaban da yake kawowa tare da kuma jan kunne game da hadurran sa.

**Rukuni na 3**

**Ziyara a matsayin garman tono ci gaba**

(1) Dole ne dukkan jama 'an da ke amfana daga ziyara su himmatu wajen kare lafiyan arzikin muhallensu don kuwa yin hakan shi zai kawo ci gaban al 'umma wanda za 'a amfana daga gareshi.

(2) Dole ne a himmatu wajen bada muhummanci ma ababen ziyara da suke inganta arzikin kasa musamman wajen ruwa da lantarta, wannan nauyin kuwa yana kan jami 'an kananan hukumomi ne da kuma manyansu.

(3) Ya kamata a dan bada tazara tsakanin lokutan ziyara Kaman wato lokutan hutu da aka fi samun maziyarta saboda kar ya zamana an takura ma muhallen ziyara da sauran ababen rayuwa na wuraren wanda yin haka zai kara ma hidiman ziyaran karko.

(4) Ya kamata kuma a tsara hidiman ziyara ta yadda ba zai zama tsanani ba ko kuma mai gurbata dawan garurrukan ziyara ta yadda ba zai zama tsanani ba ko kuma mai gurbata dawan garurrukan ziyara da kuma namun daji wanda ake tsoron yankewan rayuwarsu gaba daya a duniyan.

(5) Irin wadannan dawan da namun daji suna kara kawatar da ziyara idan har dai za a kiyaye matsanta masu.

**Rukuni na 4**

**Gudumanar da ziyara keyi wajen inganta adabin dan Adam**

(1) Dukiyan da ake ziyara dai a duniya baki daya kyauta ne ma dan adam saboda haka kula da su ya zama wajibi akan mutanen da ke wadannan muhallen.

(2) Dole ne a karimta akidodi da al 'ammuran ziyara; ya kamata a himinatu wajen inganta abadan tarihi, wuraren bauta da gidajen tarihi wanda kowane maziyarci zai iya zuwa; yana da kyau kuwa a bada karfin gwiwa ma masu ababen tarihi masu cin gashin kansu (wato ba na gwammati ba) ba tare da an muzguna musu ba ko kuma an hana su ibadar su idan wajajen ibada ne.

(3) Dole ne kuma a yi amfani da kudaden da ake samu wajen ziyara wurare don gyara da kara inganta wadannan wuraren ziyaran.

(4) ya kamata a tsara ziyara yadda ababen tarihi da deri sauran al 'adu da gargajiya musamman irin ababen da ake kerawa na gargajiya baza su shude ba su bata.

**Rukuni na 5**

**Amfanin ziyara ma kasashen da ake ziyaran.**

(1) Jami 'an wuraren da aka ziyara su taimaka ma harkan don kuwa zai zama mai samar masu da sana 'a wanda zasu raba sakamakon da aka samu a tsakanin su da adalci.

(2) Ya kamata a aiwatar da akidodin ziyaran ta yadda zasu kawo ci gaban rayuwar kowa ; tsarin wuraren sauka a ziyaran ya zama mai haddasa hadin kai wajen harkan cinikayya da kuma dai huldan yau da kullum.

(3) Dole ne a mai da hankali wajen raya wuraren da zasu iya saurin gurbata kamar muhallen ruwa da duwatsu da dai sauran wurare masu rauni wanda ziyara zai iya taimaka musu saboda rashin harkalla a irin wadannan karkarorin.

(4) Dole ne masu kasuwancin ainihin shi ziyaran (wato masu jari) su bada labari ma hukumomin ziyara akan irin binciken da suka yi da sakamakonsa akan yadda al 'ammuransu zai shafi muhallen ziyaran alal misali wato ci gaba ko kuma koma bayan da zai kawo.

**Rukuni na 6**

**Ababen da suke wajibi akan masu tafiyar da harkokin ziyara**

(1) Ya zama wajibi ne akan jami 'an ziyara su bada cikakken bayani ma maziyarta akan yanayin wurin da zasu ziyara, da irin shirin tafiyan da kuma dai irin zamantakewan da ake yi a wurin da zasu ziyarta. Dole ne ayi bayani a takardun yarjejjeniyar da shi maziyarci zai karanta, bayani kunshe da kudin da za shi biya

da kuma diyyan da za 'a biya shi idan an saba masa alkawari akan yanayin tafiyarsa.

(2) Dole ne jami 'an ziyaran su nuna damuwansu su kuma himmatu wajen kula da lafiyan maziyąrta musamman wajen tsaro, wajen hatsari wajen kula da lafiyan jiki da kuma tsabtar abinci.

(3) Yana wuyayen jami 'an ziyara su ga cewa su maziyarta sun cimma burinsu wajen ziyaran su kuma taimaka masu wajen aiwatar da addininsu.

(4) Dole ne jami 'an gwamnati da ziyara na kasar da ake ziyara su shirya yadda za 'a mai da maziyarta garinsu koda kamfanin da take gudanar da ziyaran ta fatarce.

(5) Dole ne ma gwamnati ta sanar da jama'an ta masu sha'awar ziyara su san irin hadurra da yanayi da ake tattare da kasan da suke so su ziyarta. Bai kamata a ha'inci maziyarci ba akan irin wadannan sanarwan. Sabila da haka dole ne gwamnati ta tattauna da jami'an ziyaran kasan da za'a ziyarta saboda a bada cikakken bayani ma maziyarta tun kafin kulla tafiya.

(5) Jami'an watsa labaru musamman ta hanyan amfani da na'urorin zamani suna da rawar da zasu taka wajen bada sanarwa akan ababen da suka shafi ziyara, musamman ta wajen kare lafiyan maziyarta. Ya kamata kuma suyi kokari wajen tsawatarwa akan ziyara don karuwanci.

**Yancin ziyara**

(1) ya kamata dukkan wani rayayye ya zamana yana da hanyar gane ma idonsa dukkan wurare na kayatarwa da dai kyaututuka da ubangiji ya halicci duniyan da su ba tare da wani matsala ba. Bunkasa da ake samu wajen harkan ziyara alama ce da take nuna ci gaba wajen harkan rayuwa.

(2) Yancin ziyara yana daura da yanci da mutum yake dashi don ya huta ko ya shakata, tare da iyaka wajen lokutan aiki da hutu har da ma biya kamar yadda aka bayyana a rukuni na 24 akan zayyanarwa na yancin kai da kuma rukuni na 7.d akan yarjejjeniya na yancin cinikayya da yancin kai.

(3) Ya kamata jami 'an gwamnati su bada himma wajen mara baya ma ziyara don nishadi wanda yake kawo samun tafiye – tafiye da hutu d. s. s..

(4) Ziyara irin ta iyali da ta dalibai dole ne shi ma a mara masa baya.

**Rukuni na 8**

**Iyaka wajen tafiya**

(1) Maziyarta suna da yanci su yi tafiya daga jiha zuwa jiha, daga kasa zuwa kasa, su kuma samu daman ziyaran duk wuraren da ake ziyara ba tare da an tsawwala masu ba Kaman yadda aka zayyana a rukuni na 13 akan zayyanarwa na yancin kai.

(2) Dole a ba ma maziyarta daman amfani da wasu na 'urori Kaman su talaho, su samu kuma daman ganawa da hukuma da asibiti da kuma jami 'an kasashen su da ke ofishin jakadan kasansu.

(3) Maziyarta suna da yanci dai dai da irin yadda mazauna kasa suke da shi wajen ilimin da ya shafe harkan ziyara musamman idan an ijiye ne a na 'urori Kaman su komputa.

(4) Ya kamata a aiwatar da ababen iyaka na kasashe ta hanyar da ba za 'a tsawwala ma maziyarci wajen samun yancin ketara iyaka ba.

(5) Ya kamata maziyarta su samu ikon samun dukkan irin kudin da zai zamo masu mafi sauki wajen canzarwa saboda harkan ziyaran su.

**Rukuni na 9**

**Yancin jami 'an ziyara**

(1) Ya kamata a tabbatar da tsarin albashi na jami 'an ziyara tare da hadin gwiwan gwamnati. Wannan za 'a yi shi ne tare da la 'akari da irin yanayin aikinsu ne da abun da yake bukata daga garesu.

(2) Suna da yancin neman Karin ilimi da kwarewa wajen aikin su, suna da kuma yancin neman tsari ma kansu da kuma tabbatar da aikinsu.

(3) Ko wa ma yana da yancin ya kirkori dan wani tsari ko harka a cikin hidimar ziyara matukar bai saba ma hukuma ba.

(4) Musanyan ilimi tsakanin ma 'aikatan ziyara na kasan da aka ziyarta da kuma kasan su maziyartan yana kawo inganta hidiman ziyaran baki daya.

(5) Irin masana 'antun ziyaran da suka kafu a kasashe daban daban bai kamata su tsawwala ma kasashen da suke ba. Tun da an basu yancin tafiyar da kasuwanci su

to suma ya kamata su taimaka wajen kawo ci gaban kasashen da suke kasuwancin su.

(6) Abokantaka tsakanin kamfanonin ziyara na kasanda aka ziyarta da kuma kasan maziyarta yana kawo ci gaban harkan ziyara baki daya.

(7) Ya kamata su sa tarayyan ziyara ta duniya ta buga ka 'idodin harkan ziyara na duniya su kuma yada shi duniya baki daya.

(8) Ya kamata su sa babban sakatarin tarayyan ya doshi ofishin majalisan dinkin duniya da su yi nazari akan yadda za 'a kamanta nasu ka 'idodin da na ziyara.

**Rukuni na 10**

**Aiwatar da ka 'idodin harkar ziyara na duniya**

(1) Dole ne da maziyarta da jami 'an ziyara su hada hannu wajen ganin cewa an aiwatar da wadannan ka 'idodin.

(2) Dole ne jami 'an ziyara su bada girma ma manyan ma 'aikatoti musamman ma tarayyan ziyara da sauransu wadanda suke kula da yancin kai da kare kai da lafiya na harkan ziyara.

(3) Dole ne kuwa idan aka samu sabani wajen fassara ko kuma aiwatar da ka 'idodin, to sai a kai maganan wajen kwamitin ka 'idodin ziyara.